# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: 'Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na goma: Sabon faifai


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| John: | ɗan shekara 25 |
| Jane: | 'yar shekara 25 |
| Duduwa: | 'yar shekara 35 |
| Talatu: | 'yar shekara 30 |
| Amina: | 'yar shekara 19 |
| Dije: | 'yar shekara 19 |
| Mudi: | ɗan shekara 50 |

Mataimakiyar shugaban ƙasa: 'yar shekara 55

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin shirinmu na "Ji Ka Karu" kashi na goma kuma na ƙarshe, wanda muke kawo muku a kan mutane masu ciwon taɓin hankali a nahiyarmu ta Afirka. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda aka kai yaron nan Musa wani gidan kula da yara waɗanda suka kamu da irin cutar ƙwaƙwalwar nan da ke kama mutane tun suna ƙanana, inda kuma ya haɗu da wasu yaran masu fama da irin wannan cutar. An shawarci Amina, ɗaliban nan mai koyon aikin nas da taɓin hankali ya kama ta, da ta je gidan kula da masu taɓin hankali don ta samu kulawa ta musamman. A yayin da shi kuma John wanda ya shiga hali na ƙunci da kadaici bayan ya rasa aikinshi ya dawo gida cike da murna da labarin cewa ya samu wani sabon aiki.

Bari mu ji yadda za ta kaya a cikin wannnan shiri na yau mai taken "Sabon faifai". Za mu faro shirin ne daga inda muka bar John a gidanshi tare da iyalinshi.

**Fitowa ta 1: A gidan John**

**Jane:** John, har da jaririyarmu ita ma daɗi take ji saboda ka sami wani aiki. Faɗa min mana, me ya faru? A ina za ka yi aiki? Yanzu ma a matsayin kashiya aka ɗauke ka? Nawa za a riƙa biyanka? Yaushe za ka…

**John:** Haba Malama, kwantar da hankalinki, ba ni ruwa in sha tukuna, mu zauna, kin ga sai in ba ki labarin. Abin kamar almara!

**Jane:** To, ga shi.

**John:** Yauwa! Bayan irin matsalar da na shiga a da, har na kusa sadaukar da rayuwata, amma kuma sai wata zuciya ta ce min kar in kasa a gwiwa. Kuma bayan na yi tunani sosai a

kan abin, sai na yanke shawarar zuwa shagon da ke kallon na Patel. Kin san cewa su biyu gasa suke yi a kan kwastamomi.

**Jane:** Haka ne! Ko ni ma ina zuwa shagon Patel ne kawai saboda kana zuwa aiki a can, amma kayan ɗayan shagon sun fi sauƙi.

**John:** To bari in gama. Saboda haka sai na je can, kuma kin san wani abu, ashe sun san ni! Sai na ce wa mai shagon aiki nake nema, sai ya ce min ka samu. Sai na ce mai haka kawai? Sai ya ce haka kawai. Abin sai ya ɗan ruɗa ni, sai na ce wa kaina bai kamata a ce na samu aiki da sauƙi haka ba. Saboda haka sai na ce mai, ka san wani abu kuwa, ina shan magunguna na fitar da takaici da ƙunci. Kana ganin zan iya aiki a nan?

**Jane:** A’a, sai kuma ya ce me?

**John:** Sai ya ce min ni ma haka.

**Jane:** Bai yiwuwa! Wannan mutumin na ɗaya daga cikin masu kuɗin ƙasar nan!

**John:** Ni ma abin da na yi tunani ke nan. Amma sai ya fara ba ni labarinsa. Na farko dai ya ce min ya gaji alamomin shiga cikin halin takaici ne daga iyayenshi. Saboda haka ta ɓangaren gado ke nan. Yanzu kuma yana cikin matsalar rabuwa da matarshi ne, wanda a cewar likitansa yana ɗaya daga cikin abubuwan da ke kawo shi. Daɗin daɗawa kuma, tafiyar da kasuwancinshi na shaguna da yake da su…

**Jane:** Kai! Ka ga kuwa ba wanda zai yi tsammanin cewa haka zai same shi! Ga shi yana da komai da kowa ke mafarkin samu.

**John:** Bayan wannan ma, ya ce min wai ciwon takaici ya fi sauƙin kama mata fiye da maza, saboda irin yanayinsu. Amma kuma maza sun fi saurin kashe kansu idan ciwon ya kama su.

**Jane:** Ka faɗa mai cewa ka kusa kashe kanka ne?

**John:** Kwarai da gaske, na kasa ɓoyewa. Ya faɗa min komai dangane da yadda ya yi ya ƙwaci kansa daga ciwon takaici.

**Jane:** Kai, lallai wannan babban al'amari ne! Gaskiya, ina taya ka murna da mu gaba ɗaya saboda wannan abin. Kuma ga shi saura kaɗan ma mu rasa ka.

**John:** Jane, masoyiyata! Wannan shi ne sabon faifan rayuwarmu!

**Jane:** John, masoyina! ...

**Mai ba da labari:**

Lallai dai ba kowa ba ne da ya shiga cikin hali na takaici kamar yadda John ya shiga ya yi sa'a irin wannan. Wani bincike ya nuna cewa mazaje ba sa yarda da cewa ciwon takaici ya kama su wanda kuma hakan yakan sa su ƙi neman magani.

Yanzu bari mu bar waɗannan iyalin da ke cikin farin ciki, mu garzaya gidan kula da yaran nan masu fama da ciwon ƙwaƙwalwa, wanda yanzu haka Musa ya yi makwanni da fara zuwa. Talatu, ma'aikaciyar sa-kai a ƙungiyar na da wani labari da take so ta faɗa wa mahaifiyar Musan, wato Duduwa.

**Fitowa ta 2: A gidan kula da yara masu fama da ciwon ƙwaƙwalwa**

**Duduwa:** To Talatu, kin ce akwai labarin da kike so ki faɗa min. Me ya faru?

**Talatu:** Kwarai da gaske ina da shi. Kamar yadda za ki iya tunani ya shafi Musa ne kawai.

**Duduwa:** Wani abu ya faru ne? Abin yana daɗa ƙaruwa ne?

**Talatu:** Ƙaruwa? A'a! Musa ya birge kowa da ƙoƙarinshi na iya yin zane da fenti.

**Duduwa:** Me kike nufi? Ya aka yi kika gane haka?

**Talatu:** Kamar yadda na yi miki bayani tun farko, idan aka kawo masu matsala irin wannan, a karin farko mukan yi ƙoƙarin inganta wani abu da suke son yi ne, da kuma ba su ƙwarin gwiwa ta yadda za su iya fara dogara da kansu. Muna fara yin haka ne ta hanyar fara nuna musu hanyoyin nishaɗi kamar su waƙa, da rawa, da wasan kwaikwayo, da zane, da wasannin motsa jiki, da dai sauransu. Cikin 'yan kwanaki kaɗan na gane cewa ɗanki yana da baiwa ta iya zana lambobi da yin fenti. Kalli irin abin da ya yi ta zanawa.

**Duduwa:** Kuma shi ya zana waɗannan da yi musu fenti, duk shi kaɗai?

**Talatu:** Da farko na ɗan taimake shi tun da bai san abin da ya kamata ya yi da biro da takarda ba. Amma nan da nan kuma sai ya fara yi da kanshi. Ba ki ga yadda hotunan suka yi kyau ba?

**Duduwa:** Ai ba kyau kaɗai ba, ni a wurina kuɗi ba zai iya sayensu ba! Musa ɗana, wai a ce shi ya yi zane wannan fentin da kanshi! Yanzu na yarda da cewa komai me iya wucewa ne.

**Talatu:** Muna da sauran aiki a gaba, amma dai akwai alamun nasara! Yana ɗaya daga cikin masu ƙoƙari da na fara gani tun lokacin da na fara aiki a nan. Zan ba ki shawarar ki riƙa ba shi ƙwarin gwiwa ya ci gaba da yin zane har a gida ma.

**Duduwa:** Kwarai kuwa, ƙwarai kuwa, Talatu! Na ji daɗin yadda kike kulawa da shi. Kin ga tun da ya fara zuwa nan sai ya fara natsuwa, kuma da na ga duk zane-zanen na da ya yi da kanshi sai na ji daɗi ya rufe ni. Na rasa gidana da duk abin da na mallaka, amma yanzu na yarda da cewa ɗana zai iya kuɓuta. Musa, ka bi Talatu ku tafi, zan zo in ɗauke ka an jima! Ka ji ko, ɗana?!

**Mai ba da labari:**

Yaran da ciwon ƙwaƙwalwa ya kama suna iya samun wata baiwa ta musamman wanda har yanzu masu 'yan kimiyya da masu bincike ba su iya ganewa ba. Musa na ɗaya daga cikin irin waɗannan yaran. Yanzu kuma bari mu ƙyale Musa mu koma asibitin masu taɓin hankalin nan inda Amina ke samun kulawa. Bayan makwanni biyu an yarje wa Dije ta ziyarci ƙawarta a asibitin.

**Fitowa ta 3: A asibitin masu taɓin hankali**

**Dije:** Wai...na dai kawo, tun da na yi ƙoƙari na wuce manyan ƙofofin. Yanzu saura in nemi inda Amina take kawai. ... Ikon Allah! Ni ban sa ran ganin marasa lafiya da yawa haka ba. Daga ina waɗannan mutanen suke fitowa haka? Kuma

me yake damunsu haka? Yauwa, ɗaki na goma sha ɗaya, nan ɗakin ya kamata a ce Amina take ciki. ... Amina, ni ce, Dije! In shigo? Shi ke nan, ga ni nan shigowa. An ce ba komai in shigo. … Wayyo Allahna!

**Amina da Likita:** Hehehe!! Mun bashe ta!!

**Dije:** Allah! Kun tsorata ni!

**Likita:** Ke, kwantar da hankalinki, ba wani abu.

**Amina:** Ki yi haƙuri ƙawata, ban so in ba ki tsoro ba, amma likita ne ya dage. Kuma shi ne ya ƙara hana ki ganina. Ya ce haka yana ɗaya daga cikin hanyoyin samun sauƙina.

**Likita:** Kuma an samu nasara. Har yanzu Amina tana jin waɗannan muryoyin, amma yanzu tana iya daurewa ta danne su. Ta haka ne za ta iya cin ƙarfin wannan ciwon. Magungunan da take sha suna da ƙarfi sosai, amma tana buƙatar wanda zai riƙa kulawa da ita a kai-a kai.

**Dije:** Amina, tun da kika fara samun matsalar nan ban taɓa ganin hankalinki ya kwanta ba kamar yau.

**Likita:** Magungunan da take sha ne suka taimaka wajen haka. Shi ya sa yake da muhimmanci a riƙa sa mata ido sosai. Saboda idan ta yi kuskure ta sha maganin fiye da yadda aka ƙayyade mata, to za ta iya samun matsala. Kamar yadda na ce, zan yi iyakar ƙoƙarina don in ga cewa Amina ta samu lafiya. Ba tabbaci a kan wannan, amma dai da taimakon Allah da kuma juriya za a samu nasara.

**Mai ba da labari:**
Dr. Mudi ya yi gaskiya. Ya daɗe yana zama cikin baƙin cikin ganin yadda jama'a suke kallon masu taɓin hankali a matsayin wasu dabbobi. Amma dai abubuwa na da alamun canzawa.
'Yan kwanaki kaɗan bayan nan, mataimakiyar shugaban ƙasar wadda kuma ita ce ministan kuɗi ta ƙasar tana sanar da yadda kasafin kuɗin ƙasar ya kasance. Bari mu kasance da ita a zauren majalisar wannan ƙasar.

**Fitowa ta 4: A majalisa**

**Mataimakiyar shugaban ƙasa:** Na gode, 'yan'uwana. Yanzu kafin in karanto abu na gaba a kasafin kuɗi, ku ba ni dama in ce wani abu. Mun yanke shawarar mu ƙara kasafin kuɗin ɓangaren kiwon lafiya, musamman ma ta ɓangaren masu taɓin hankali da kuma nakasassu da ƙarin kashi hamsin bisa kuɗin da aka kashe a shekarar bara.

**Mai gabatarwa:**
Da wannan sanarwa kuma muka kawo ƙarshen shirinmu na "Ji Ka Karu" a kan masu taɓin hankali a nahiyar Afirka. Chrispin Mwakideu ne ya rubuta labarin. Kuma muna fata kun ji daɗin sauraro. A tuna cewa ana iya ƙara sauraron dukkan shirye-shiryen namu a adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kuma muna marhabin da ku a shafinmu na Facebook domin muhawar ko tofa albarkacin bakinku. Sai kuma mun ƙara saduwa a cikin wani sabon shirin. Ku huta lafiya!

**’Yan Wasa:**

Munir Isa

Ruƙayyatu Bala

Maryam Ibrahim

Buhari Mohammed Ibrahim

Ado Abdulkadir

Zainab Bala

Ɗan Fulani

Kabiru Mohammed

Habiba Inuwa

Aishatu Modibbo Wali

Umar Sherrif

Yusuf Idris

Abu Hassan

Yunusa Musa

Auwal Sherrif